*2.* To, me ya sanar da ƙai abin da ake cewa Lailatul Ƙadari?

*3.* Lailatul Ƙadari mafi alheri ne daga wasu watanni dubu.

*4.* Mala'iku da Rũhi suna sauka a cikinsa da iznin Ubangijinsu sabõ-da kowane umurni.

*5.* Sallama ne shi daren, har fitar alfijiri.

وَمَآ أَدۡرَىٰكَ مَا لَيۡلَةُ ٱلۡقَدۡرِ ٢

لَيۡلَةُ ٱلۡقَدۡرِ خَيۡرٞ مِّنۡ أَلۡفِ شَهۡرٖ ٣

تَنَزَّلُ ٱلۡمَلَٰٓئِكَةُ وَٱلرُّوحُ فِيهَا بِإِذۡنِ رَبِّهِم مِّن
كُلِّ أَمۡرٖ ٤

سَلَٰمٌ هِيَ حَتَّىٰ مَطۡلَعِ ٱلۡفَجۡرِ ٥

## SŨRATUL BAYYINA سُورَةُ البَيِّنَةِ

Tana karantar da hãlãyen kãfirai da mutãnen Littãfi, wãto Yahũdu da Nasãra game da Annabi, tsĩra da amincin Allah su tabbata a gare shi, a gabanin da bayan bayyanarsa.

بِسۡمِ ٱللَّهِ ٱلرَّحۡمَٰنِ ٱلرَّحِيمِ

*Da sũnan Allah, Mai rahama, Mai jin ƙai.*

*1.* Waɗanda suka kãfirta daga mũtanen Littafi, da mushirikai, ba su kasance mãsu gushewa daga gaskiya ba har hujja ta je musu.

*2.* Wani Manzo[1] daga Allah, yana karãtun wasu takardu masu tsarki.

لَمۡ يَكُنِ ٱلَّذِينَ كَفَرُواْ مِنۡ أَهۡلِ ٱلۡكِتَٰبِ وَٱلۡمُشۡرِكِينَ
مُنفَكِّينَ حَتَّىٰ تَأۡتِيَهُمُ ٱلۡبَيِّنَةُ ١

رَسُولٞ مِّنَ ٱللَّهِ يَتۡلُواْ صُحُفٗا مُّطَهَّرَةٗ ٢

(1) Shi ne Muhammadu, tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi, dõmin bãbu wanda ya dãce da abin da ke cikin littafansu sai shi.

*3.* A cikinsu akwai wasu littafai mãsu ƙīma da daraja.

فِيهَا كُتُبٌ قَيِّمَةٌ ٣

*4.* Kuma waɗanda aka bai wa Littafi ba su sãɓa wa juna ba face bayan hujjar ta je musu.

وَمَا تَفَرَّقَ ٱلَّذِينَ أُوتُوا۟ ٱلْكِتَـٰبَ إِلَّا مِنۢ بَعْدِ مَا
جَآءَتْهُمُ ٱلْبَيِّنَةُ ٤

*5.* Kuma ba a umarce su da kome ba, fãce bautã wa Allah, suna mãsu tsarkake addinin gare Shi, mãsu karkata zuwa ga addinin gaskiya, kuma su tsai da salla kuma su bãyar da zakka, kuma wannan shi ne addinin waɗanda suke a kan hanyar ƙwarai.

وَمَآ أُمِرُوٓا۟ إِلَّا لِيَعْبُدُوا۟ ٱللَّهَ مُخْلِصِينَ لَهُ
ٱلدِّينَ حُنَفَآءَ وَيُقِيمُوا۟ ٱلصَّلَوٰةَ وَيُؤْتُوا۟
ٱلزَّكَوٰةَ ۚ وَذَٰلِكَ دِينُ ٱلْقَيِّمَةِ ٥

*6.* Lalle ne waɗanda suka kafirta daga mutanen Littafi da mushirikai suna cikin wutar Jahannama, suna madawwama a cikinta. Waɗannan su ne mafi ashararancin tãlikai.

إِنَّ ٱلَّذِينَ كَفَرُوا۟ مِنْ أَهْلِ ٱلْكِتَـٰبِ
وَٱلْمُشْرِكِينَ فِى نَارِ جَهَنَّمَ خَـٰلِدِينَ فِيهَآ ۚ أُو۟لَـٰٓئِكَ
هُمْ شَرُّ ٱلْبَرِيَّةِ ٦

*7.* Lalle ne waɗanda suka yi īmãni, kuma suka aikata ayyukan ƙwarai, waɗannan su ne mafifita alherin halitta.

إِنَّ ٱلَّذِينَ ءَامَنُوا۟ وَعَمِلُوا۟ ٱلصَّـٰلِحَـٰتِ
أُو۟لَـٰٓئِكَ هُمْ خَيْرُ ٱلْبَرِيَّةِ ٧

*8.* Sakamakonsu, a wurin Ubangijinsu, shi ne gidajen Aljannar zama, ƙoramu na gudãna daga ƙarƙashinta, sunã madawwama a cikinta har abada. Allah Ya yarda da su, kuma su, sun yarda da Shi. Wannan sakamako ne ga wanda ya ji tsõron Ubangijinsa.

جَزَآؤُهُمْ عِندَ رَبِّهِمْ جَنَّـٰتُ عَدْنٍ تَجْرِى
مِن تَحْتِهَا ٱلْأَنْهَـٰرُ خَـٰلِدِينَ فِيهَآ أَبَدًا ۖ رَّضِىَ ٱللَّهُ
عَنْهُمْ وَرَضُوا۟ عَنْهُ ۚ ذَٰلِكَ لِمَنْ خَشِىَ رَبَّهُۥ ٨